# TAMBAYA 100 DA AMSARSU

TARAWA DA TANADA

ABDUL' AZIZ IBNU MUHAMMAD AL-SHA' ALAN



FASSARA: ISMA' IL GARBA ALI | BITA: TAJUDDIN ISA

# 100

# سُؤَالٍ وَجوَابُهُ

# (فِي عَقِيدةِ التَّوْحِيدِ)


جمع وإعداد:

## عبد العزيز بن محمد الشعلان

مدير المكتب التعاوني للدعوة والإرشاد

وتوعية الجاليات بحي العزيزية بالرياض


ترجمة: إسماعيل غرب علي

مراجعة: تاج الدين عيسى

# TAMBAYA 100 DA AMSARSU
# (A CIKIN AKIDAR TAUHIDI)

**TARAWA DA TANADA**

**ABDUL'AZIZ IBNU MUHAMMAD AL-SHA'ALAN**

DARAKTAN OFISHIN DIN TAIMAKEKENIYA

DAN DA'AWA DA SHIRYARWA

DA WAYAR DA KAN BAKI MAZAUNA SAUDIYYA A UNGUWAR AZIZIYYA RIYADH

FASSARA: ISMA'IL GARBA ALI

BITA: TAJUDDIN ISA




**DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINƘAI**

## DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JIN KAI

**Godiya ta tabbata ga Allah; bayan haka:**

Na karanta wadan nan tambayoyi da amsa wadanda babban malami Abdu'aziz ibnu Muhammad al-Sha'alan ya rubutasu, kuma ya kunsa musu littafin "Salasatil Usul da al-Kawa'idul Arba'i" na babban malami shugaba mujaddadi Muhammad ibnu Abdulwahhab – Allah Yayi masa rahama -, sai na samu hakan aiki ne mai kyau mai bada fa'ida zai taimaka akan sanin wannan littafin mai girma, kuma zai kusantar da shi dan fahimtarwa, Allah Yayi masa sakayya da alheri kuma Ya anfanar da iliminsa.

Wanda ya rubutashi

**Saleh ibnu Fauzan al-Fauzan**

Memba a kwamitin manyan malamai

A 21/3/1440 H

## DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JIN KAI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangjin talikai, tsira da aminci su tabbata ga madaukakin Annabwa da manzanni, bayan haka:

Wadan nan wasu tambayoyi ne da amsoshinsu a asalin asalillika shine kadaita Allah – tsarki ya tabbatar maSa -, da gargadarwa daga kishiyarsa shine yiwa Allah shirka da hanyoyinta, da kuma kudirin Ahlussunnah wal jama’a, na tsagosu ta takaitacciyar hanya, na kiyaye dan su zama masu saukin fahimta ga mai karatu.

Ina rokon Allah – tsarki ya tabbatar maSa – Ya anfanar da su.

**Abdul’aziz ibnu Muhammada al-Sha’alan**

Daraktan ofis din taimakekeniya dan yin da’awa da shiryarwa

Da wayar da kan baki mazauna Saudiyya a unguwar Aziziyya a Riyadh

## AKIDAR TAUHIDI TAMBAYA DA AMSARTA

**TAMBAYA TA 1: Me yasa muke karanta Tauhidi?**

**AMSA TA 1**: Domin shine asalin asalillika, kuma saboda shi ne Allah Ya halicci aljanu da mutane, kuma Allah Ya aiko manzanni, Ya saukar da littatttafai, kasuwar aljanna da wuta suka tsaya, mutane suka rabu zuwa musulmai da kafirai, Allah – Madaukakin sarki – Ya ce: ***{Ban halicci aljanu da mutane ba sai dan su bauta Mini}*** [al-Zariayt: 56].

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 2: Daga ina zamu dauki akidarmu?**

**AMSA TA 2:** Daga al-Kur'ani da sunna da kuma abinda magabata na kwarai suke akansa.

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 3: Menene tushe uku wadanda saninsu yake wajaba akan mutum, kuma wadanda za'ayi tambaya game da su a cikin kabari?**

**AMSA TA 3:** Bawa yasan Ubangijinsa, da Addininsa, da Annabinsa Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -.

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 4: Waye Ubangijinka?**

**AMSA TA 4:** Ubangijina Shine Allah wanda Ya reneni, kuma Ya reni dukkan talikai da ni'imominSa, Shine abin bautawa bani da wani abin bauta inba Shi ba, dalili shine fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai}*** [al-Fatiha: 2].

**TAMBAYA TA 5: Da me kasan Ubangijinka?**

**AMSA TA 5:** Na sanShi da ayoyinSa da halittunSa, daga ayoyinSa: Dare da yini, da rana da wata, daga halittunSa: Sammai bakwai da abinda ke cikinsu, da kassai bakwai da abinda ke cikinsu, da abinda ke tsakaninsu, dalili fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Daga ayoyinSa dare da yini da rana da wata, kada kuyi sujjada ga rana ko ga wata kuyi sujjada ga Allah wanda Ya halicce su in kun kasance Shi kuke bautawa}*** [Fussilat: 37].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 6: Ina Allah Yake?**

**AMSA TA 6:** A sama Ya daidaita akan Al'arshi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 7: Menene dalili daga al-Kur'ani akan cewa Allah – tsarki ya tabbatar maSa – Yana sama kuma Shi Yana kan al'arshi?**

**AMSA TA 7:** Dalilin cewa Shi Yana sama fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Shin kun amnice wanda ke cikin sama}*** [al-Mulk: 16].

Kuma dalili akan cewa Shi Yana kan al'arshi fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Mai rahama Ya daidaita akan al'arshi}*** [Daha: 5]. A gurare bakwai daga littafinSa.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 8: Menene ma'anar (Ya daidaita)?**

**AMSA TA 8:** Ya daukaka Yayi sama Ya hau Ya tabbata.

**TAMBAYA TA 9: Saboda me Allah Ya halicci aljan da mutum?**

**AMSA TA 9:** Dan bautarSa Shi kadai baShi da abokin tarayya.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 10: Menene dalili daga al-Kur'ani akan cewa Allah Ya halicci aljani da mutum dan bautarSa?**

**AMSA TA 10:** FadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Ban halicci mutum da aljani ba sai dan su bauta Mini}*** [al-Zariyat: 56].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 11: Menene ma'anar {Su bauta Mini}**

**AMSA TA 11:** Su kadata Ni.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 12: Mecece ibada?**

**AMSA TA 12:** Ita sunane mai tattaro dukkan abinda Allah Yake sonsa kuma Ya yarda da shi na maganganu da ayyuka na zahiri da badini.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 13: Menene ma'anar shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah?**

**AMSA TA 13:** Wato: Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 14: Menene ma'anar shaidawa Annabi Muhammad Manzon Allah ne?**

**AMSA TA 14:** Yi masa biyayya a cikin abinda yayi umarni da shi, da gasgatashi a cikin abinda ya bada labari, da nisantar abinda yayi hani

daga gare shi kuma ya tsawatar, kuma kada a bautawa Allah sai da abinda ya shara'anta.

---------------------------------------------

**TAMBAYA TA 15: Menene mafi girman abinda Allah – Madaukakin sarki - Yayi umarni da shi?**

**AMSA TA 15:** Mafi girman abinda Allah Yayi umarni da shi shine Tauhidi shine bauta maSa Shi kadai baShi da abokin tarayya, Madaukakin sarki Ya ce: ***{Hakika mun aiko wani manzo a kowace al'umma cewa a bautawa Allah kuma a nisanci dagutu}*** [al-Nahl: 36].

---------------------------------------------

**TAMBAYA TA 16: Menene rabaraben Tauhidi?**

**AMSA TA 16:** Tauhidur Rububiyyah, da Tauhidul Uluhiyya, da Tauhidin sunaye da siffofi.

---------------------------------------------

**TAMBAYA TA 17: Menene ta'arifin Tauhidur Rububiyyah?**

**AMSA TA 17:** Kadaita Allah a cikin ayyukanSa misali: Halitta da azirtawa da saukar da ruwa…zuwa karshe.

---------------------------------------------

**TAMBAYA TA 18: Menene ta'arifin Tauhidul Uluhiyya?**

**AMSA TA 18:** Kadaita Allah da ayyukan bayi wadanda Ya shara'anta musu, misali: Addu'a, da yanka, da sujjada.

**TAMBAYA TA 19: Menene ta'arifin Tauhidin sunaye da siffofi?**

**AMSA TA 19:** Shine kadaita Allah – tsarki ya tabbatar maSa – da abinda Ya kebanceShi na sunaye da siffofi. Madaukakin sarki Ya ce; ***{Babu wani abu tamkarSa Shi mai ji ne kuma Mai gani ne}*** [al-Shura: 11].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 20: Ka ambaci wasu daga nau'ikan ibada?**

**AMSA TA 20:** Daga nau'ikanta: Addu'a da neman agaji, da neman taimako, da yanka abin neman kusanci, da bakance, da tsoro, da kauna, da dogaro, da komawa, da soyayya, da razani, da kwadayi, da firgita, da ruku'u da sujjada, da khushu'i, da kankar da kai, da karatun al-Kur'ani.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 21: Menene mafi girman abinda Allah Yayi hani daga gare shi?**

**AMSA TA 21:** Mafi girman abinda Yayi hani daga gareshi itace shirka, itace bautar wanin Allah tare da Allah, Madaukakin sarki Ya ce: ***{Lallai Allah baYa gafarta ayi shirka da Shi Yana gafarta koma bayan haka ga wanda Ya so}*** [al-Nisa'i: 48].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA 22: Menene nau'ikan shirka?**

**AMSA TA 22:** *Nau'i na farko:* Shirka babba: Itace Dukkan abinda Allah da manzonSa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – suka ambace shi shirka, kuma ya fitar da ma'abocinsa daga Musulunci, misali: Bautar gumaka da matattu, da yin sujjada ga wanin Allah.

*Nau'i na biyu:* Karamar shirka: Itace dukkan abinda yazo a shari'a cewa shirka ne, amma bai fitar da ma'abocinsa daga Musulunci ba, misali: Rantsuwa da wanin Allah, da sassaukar riya, da fadin: Allah Ya so da kai. An anbaceshi shirka karama domin cewa shi hanya ce ta fadawa babbar shirka.

-----------------------------------------------

**TAMBAYA TA 23: Yaushe ne shirka ta farko ta afka cikin mutane?**

**AMSA TA 23:** Farkon sharkar da ta fara afkawa a cikin mutane, ta afka ne a cikin mutanen Annabi Nuhu – aminci ya tabbata agare shi -.

-----------------------------------------------

**TAMBAYA TA 24: Menene sababin afkuwar shirka a cikin mutane Annabi Nuhu – aminci ya tabbata agare shi -?**

**AMSA TA 24:** Sababi shine: Wuce gona da iri a sha'anin salihai.

-----------------------------------------------

**TAMBAYA TA 25: Menene ma'anar wuce gona da iri a sha'anin salihai?**

**AMSA TA 25:** Shine kari a cikin yabonsu, da dagasu sama da matsayinsu, shine a juyar da wani abu na bauta garesu, dalili fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Yaku mazowa littafi kada ku wuce gona da iri a cikin Addininku}*** [al-Nisai'i: 171]. Kuma tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: *"Kada ku zirfafa a yabona kamar yanda Nasara suka zirfafa a Isa dan Maryam, kadai ni bawan Allah ne, to kuce: Bawan Allah kuma ManzonSa".* Bukhari ne ya ruwaito shi. Ma'anar (Kada ku zirfafa a yabona) wato: Kada kuyi kari a cikin yabona.

**TAMBAYA TA 26: Menene hukuncin kiran matattu?**

**AMSA TA 26:** Kiran matattu da wasunsu a cikin abinda ba wanda yake da iko akansa sai Allah to shirka ne babba yana fitarwa daga Musulunci, dalili daga al-Kur'ani: ***{Wanda ya kira tare da Allah wasu abubuwan bautawa daban to bashi da wata hujja game da shi (kiran) to hisabinsa yana wurin Ubangijinsa kawai, lallai cewa shi kafirai basu cin nasara}*** [al-Muminun: 117].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 27: Shin rokon Allah yana bukatar tsanin wani abin halitta?**

**AMSA TA 27:** Addu'a bata bukatar tsanin wani abin halitta, dalili fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Idan bayiNa suka tambayeka game da Ni to lallai cewa Ni makusanci ne, ina amsa kiran mai kira idan ya kiraNi}*** [al-Bakara: 186].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 28: Shin matattu suna amsa kira?**

**AMSA TA 28:** Matattu basa amsa kira; dalili fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Idan kun kirasu baza suji kiranku ba, koda sunji to bazasu amsa muku ba, kuma ranar alkiyama zasu butulcewa shirkarku}*** [Fadir: 14].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 29: Danwa zamuyi yanka kuma muyi sallah?**

**AMSA TA 29:** Ga Allah Shi kadai baShi da abokin tarayya, Madaukakin sarki Ya ce: ***{Kayi sallah ga Ubangijinka kuma ka soke (baiko wato sukar rakumi)}*** [al-Kausar: 2].

**TAMBAYA TA 30: Menene hukuncin yanka da sujjada ga wanin Allah?**

**AMSA TA 30:** Shirka ce babba mai fitarwa daga Addinin Musulunci.

Madaukakin sarki Ya ce: ***{Kace lallai salallata da baikona, da rayuwata da mutuwata duk suna ga Allah Ubangijin talikai* Bashi da abokin tarayya, da wancan ne aka umarce ni kuma nine farkon masu sallamawa}*** [al-An'am: 162,163]. (ibadata): wato yanka na.

**TAMBAYA TA 31: Menene hukuncin rantsuwa da wanin Allah; misali rantsuwa da Annabi – tsira da amincin Allah su tabbat agare shi – ko da amana ko da daukaka ko waninsu?**

**AMSA TA 31:** Hukuncinsa: Shirka ce karama.

Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: *"Wanda zaiyi rantsuwa to ya rantse da Allah ko yayi shiru".* Bukhari ne ya ruwaito shi.

---

**TAMBAYA TA 32: Menene wajibi akan musulmi a bangaren sunayen Allah da siffofinSa?**

**AMSA TA 32:** Tabbatar da abinda Allah Ya tabbatarwa kanSa, ko ManzonSa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya tabbatar masa, da kore abinda Allah Ya korewa kanSa, ko ManzonSa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya kore maSa, na sunayenSa da siffofinSa – tsarki ya tabbatar maSa Ya daukaka – ba tare da canjawa ba ko korewa da kamantawa ko misaltawa ba.

**TAMBAYA TA 33: Menene dalili daga al-Kur'ani akan cewa siffofin Allah basuyi kama da siffofinmu ba?**

**AMSA TA 33:** Fadinsa – Madaukakin sarki -: ***{Babu wani abu tamkarSa, Shine Mai yawan j kuma Mai yawan gani}*** [al-Shura: 11].

**---------------------------------------------**

**TMBAYA TA 34: Menene Addininka?**

**AMSA TA 34:** Addinina shine Musulunci; dalili fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Lallai Addini a wurin Allah shine Musulunci}*** [Aal-Imran: 19].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 35: Shin Allah Yana karbar wani Addinin ba Musulunci ba bayan aiko Annabi Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -?**

**AMSA TA 35:** Allah baYa karbar wani Addini wanda ba Musulunci ba bayan aiko Manzo – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -; dalili shine fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Wanda ya nemi wani Addini wanin Musulunci to baza'a karba daga gareshi ba kuma shi a lahira yana daga masu hasara}*** [Aal-Imran: 85].

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 36: Menene ta'arifin Musulunci?**

**AMSA TA 36:** Shine mika wuya ga Allah da Tauhidi, da jawuwa gareShi da biyayya, da barranta daga shirka da ma'abotanta.

**TAMBAYA TA 37: Menene rukunan Musulunci?**

**AMSA TA 37:** Shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma Annabi Muhammada – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ManzonSa ne, da tsaida sallah, da bada zakka, da azimin Ramadan, da ziyartar Daki ga wanda ya samu ikon zuwa gareshi.

Dalili shine fadinSa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi –: *"Musulunci shine ka shaida cewa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma cewa Annabi Muhammad Manzon Allah ne, ka tsaida sallah, ka bada zakka, ka azimci Ramadan, ka ziyarci Daki idan ka samu ikon zuwa gare shi"* Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 38: Menene ta'arifin imani?**

**AMSA TA 38:** Shine: Fada da harshe, da kudircewa da zuciya, da aiki da gabbai, yana karuwa da biyayya, kuma yana raguwa da sabo.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 39: Menene rukunan imani?**

**AMSA TA 39:** Imani da Allah da mala'ikunSa da littattafanSa da ManzanninSa da ranar lahira, kuma kayi imani da kaddara alherinsa da sharrinsa" Muslim ne ya ruwaito shi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 40: Su waye mala'iku?**

**AMSA TA 40:** Mala'iku wata duniya ce ta boye Allah Ya halicce su dan bautarSa.

**TAMBAYA TA 41: Menene hukuncin imani da mala'iku?**

**AMSA TA 41:** Wajibi ne, ba'a karbar imani sai da shi.

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 42: Waye mafificin mala'iku?**

**AMSA TA 42:** Jibril – aminci ya tabbata agare shi, shi aka wakilta da saukar da wahayi.

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 43: Wadan nene littattafan sama?**

**AMSA TA 43:** Sune littattafan da Allah Ya saukar da su ga ManzanninSa – aminci ya tabbata agare su -, misali: Attaura da Linjila da Zabura da al-Kur'ani.

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 44: Menene hukuncin imani da littattafai?**

**AMSA TA 44:** Wajibi ne, ba'a karbar imani sai da shi.

**----------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 45: Wannan ne mafi girman littattafan sama?**

**AMSA TA 45:** Mafi girman littattafai: Shine al-Kur'ani mai girma wanda Allah Ya saukar da shi ga Annabi Muhammada – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -.

Shi mai shafe dukkan littattafan sama ne, bautawa Allah baya halatta sai da shi. Madaukakin sarki Ya ce: ***{Mun saukar maka da littafi da gaskiya mai gasgatawa ne ga abinda ke gabansa daga littafi kuma mai rinjaye ne akansa}*** [al-Ma'ida: 48].

**TAMBAYA TA 46: Mecece ranar lahira?**

**AMSA TA 46:** Itace ranar al-Kiyama wacce za'a tashi mutane a cikinta dan yin hisabi da sakayya.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 47: Menene hukuncin imani da ranar lahira?**

**AMSA TA 47:** Wajibi ne, ba'a karbar imani sai da shi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 48: Menene ma'anar imani da kaddara?**

**AMSA TA 48:** Kaddara: Itace kaddarawar Allah ga halittu gwargwadan abinda saninSa ya rigaya da shi, kuma hikimarSa ta hukunta shi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 49: Menene hukuncin imani da kaddara?**

**AMSA TA 49:** Wajibi ne, ba'a karbar imani sai da shi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 50: Menene kyautayi?**

**AMSA TA 50:** Kyautayi: Shine ka bautawa Allah kamar kana ganinSa, idan kai baka ganinSa to lallai Shi Yana ganinka.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 51: Menene ta'arifin riya?**

**AMSA TA 51:** Riya: Itace yin bauta saboda mutane su ganshi su yabeshi.

**---------------------------------------------**

**TAMBAYA TA 52: Menene hukuncin riya?**

**AMSA TA 52:** Riya abar haramtawa ce, kuma ita tana daga shirka karama.

Dalili shine fadinsa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: *"Mafi tsoron abinda nake jiye muku tsoro karamar shirka" sai aka tambaye shi game da ita sai ya ce: "Riya".* Ahmad ne ya ruwaito shi kuma Albani ya inganta shi.

---------------------------------------------

**TAMBAYA TA 53: waye Annabinka?**

**AMSA TA 53:** Annabina shine: Muhammad dan Abdullahi da AbdulMuddalib dan Hashim, Hashim daga Kuraish ya ke, Kuraish kuma daga Kinana ne, Kinana daga Larabawa suke, Larabawa kuma daga zuriyar Annabi Isma'il ne, Annbai Isma'il dan Annabi Ibrahim ne – aminci ya tabbata agare shi -.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 54: Menene mafi girman dalilan Annabcinsa?**

**AMSA TA 54:** Mafi girman dalilan Annabcinsa shine al-Kur'ani mai girma, shi zancen Allah ne wanda shine shiriya da waraka da haske.

Allah Madaukakin sarki – Ya ce: ***{Kace da ace mutane da aljanu zasu taru akan suzo da kwatankwacin wannan al-Kur'anin bazasuzo da kwatankwacinsa ba koda sashinsu mai taimakon sashi ne}*** [al-Isra'i: 88].

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 55: Mene ne mafi girman hakkokin Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -?**

**AMSA TA 55:** Daga mafi girman hakkokin Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: Yin imani na gaskiya da shi – aminci ya tabbata agare shi -, kuma cewa Allah Ya aikoshi ga aljanu da mutane baki daya, da wajabcin yi masa biyayya, da gargadarwa daga sabonsa, da binsa da koyi da shi, da girmama sunnarsa, da sonsa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi –sama da iyalai da 'ya'ya da mutane baki daya, da girmama shi, da ganin alfarmarsa, da yin salati gareshi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – da rashin wuce gona da iri da daukakashi sama da matsayinsa wanda Allah Ya saukar da shi a cikinsa.

**---------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 56: Menene tsafi?**

**AMSA TA 56:** Tsafi: Shi wani aiki ne na Shaidan da yake tasiri a cikin zukata da jikkuna a hakika, daga cikinsa akwai raye-rayen da suke tasiri a idanuwa wadanda ba hakika bane.

**---------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 57: Menene bokanci?**

**AMSA TA 57:** Bokanci shine: Da'awar sanin gaibu ta hanyar anfani da aljani.

**---------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 58: Waye dan duba?**

**AMSA TA 58:** Dan duba: Shine wanda yake da'awar sanin al'amuran dake boye da wasu mukaddimar da yake kafa hujja da ita akan abinda aka sace da gurin da abu ya bata.

Ance: Dan duba suna ne na boka da masanin taurari da dan ramli da makancinsu, daga wadanda suke magana a cikin sanin al'amuran dake boye ta hanyar aljanu. Daga ayyukansu: Anfani da taurari, da karatu a tafi, da kofuna, da kafa hujja da wdan nan abubuwan akan al'amuran da ke boye.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 59: Menene hukuncin tafiya wajen dan duba da boka da wasunsu daga wadanda suke da'awar sanin ilimin gaibu?**

**AMSA TA 59:** Haramun ne tafiya zuwa gurin matsafi da dan duba da boka, a cikin "Sahihu Muslim" akwai fadin Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: *"Wanda yazowa dan duba sai ya tambayeshi daga wani abu, sai ya gasgatashi, baza'a karbi sallarsa ta dare arba'in ba".*

Daga Abu Huraira – Allah Ya yarda da shi -, daga Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: *"Wanda yaje wajen dan duba ko boka, sai ya gasgatashi a cikin abinda ya fada; to hakika ya kafircewa abinda aka saukarwa Annabi Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi –"*. Ahmad ne da Abu Dawud da Tirmizi suka ruwaito shi.

**TAMABAYA TA 60: Mennene hukuncin tsafi da koyansa?**

**AMSA TA 60:** Tsafi dukkansa haramun ne kuma kafirci ne, koyonsa da kuma koyar da shi, ba'a halatta komai ba daga gare shi ba, Madaukakin sarki Ya ce: ***{(Annabi) Sulaiman bai kafirta ba sai dai cewa shaidanu sun kafirta suna koyar da mutane tsafi}*** Aya [al-Bakara: 102].

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 61: Menene hukuncin karanta burajan rabo da abinda zai faru nan gaba da kuma gasgata su?**

**AMSA TA 61:** Su suna daga ayyukan mutanen Jahiliyya, kuma su masu shiga ne cikin gasgata ‘yan duba da masana taurari a cikin da’awar sanin gaibu, tsira da amincin Allah su tabbata aage shi – ya ce; *“Wanda ya nemi wani yanki daga taurari to hakika ya nemi wani yanki na sihiri, muddin ya kara neman wani yanki na sanin taurari ya kara sanin wani yanki na tsafi”* Abu Dawud ne ya ruwaito shi kuma sanadinsa ingantacce ne.

**---------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 62: Menene ta’arifin layu?**

**AMSA TA 62:** Layu: jam’i ne na laya, itace wasu kulle-kulle ko kasusuwa ko rubuce-rubuce, ko fatu ko dinke-dinke ko gyale ko wasunsu, ana ratayawa yara su a wuya, ko a damattsa, ko a gidaje ko motoci, da manufar tunkude bala’i kafin faruwarsa, ko dauke shi bayan afkuwarsa.

**---------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 63: Menene hukuncin layu?**

**AMSA TA 63:** Shirka ne karama, zata iya zama babba idan ya kudirce cewa su zasu anfanar ko zasu cutar koma bayan Allah.

Dalili shine fadinsa – tsira da aminci su tabbata agare shi -: *“Wanda ya rataya laya to hakika yayi shirka”.* Ahmad ne ya ruwaito shi kuma Albani ya inganta shi.

**---------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 64: Mecece tawada ta shari'a, kuma menene hukuncinsu?**

**AMSA TA 64:** Itace karantawa mara lafiya al-Kur'ani ko addu'o'i, da tofi akan gurin da yake radadi. Tawada ta halatta, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: "*Babu laifi da tawada muddin dai ba shirka ba ce*". Muslim ne ya ruwaito shi.

An sharadanta halaccinta ta kadaita daga shirka, kuma a kudirce cewa ita bata tasiri da kanta, kai ita wani sababi ce, anfanarwa da cutarwa suna hannun Allah – tsarki ya tabbatar maSa – kuma ta kasance da harshen larabci ko da abinda ake sanin ma'anarsa daga wanin larabci, kuma ta kasance da zancen Allah ko da sunayenSa da siffofinSa.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 65: Menene canfi?**

**AMSA TA 65:** Canfi: Shine fata ko canfi da tsuntsaye.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 66: Menene hukuncinsa? tare da dalili?**

**AMSA TA 66:** Haramun ne, kuma shi yana daga shirka karama, zai iya zama shirka babba idan ya kudirce cewa shi yana anfanarwa ko yana cutarwa koma bayan Allah, dalili shine fadinsa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: *"Canfi shirka ne"* Ahmad ne da Adu Dawud suka ruwaito shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 67: Shin canfi yana faruwa ba tare da tsuntsaye ba?**

**AMSA TA 67:** Eh, misali: Canfi da wasu daga watanni, ko kwanuka, ko dabbobi, ko wasu daga ma'abota siffofi na jiki; kamar makaho, da gurgu, da wasunsu.

**----------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 68: Menene ma'anar neman shayar da ruwa da masaukan taurari?**

**AMSA TA 68:** Ma'anar neman shayar da ruwa da masaukan taurari: Wato: Neman saukar ruwa daga taurari, da danganta ruwan garesu idan ya sauka.

**----------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 69: Menene hukuncin neman shayar da ruwa da masaukan taurari?**

**AMSA TA 69:** Shi ya rabu gida biyu:

*Na farko:* Ya kudirce cewa taurari sune suke saukar da ruwa, to wannan kafirci ne; domin cewa shi shirka ne da Allah – tsarki ya tabbatar maSa -.

*Na biyu:* Ya kudirce cewa Allah Shine wanda Yake halittar ruwa kuma Yake saukar da shi, sai dai cewa yana kudirce cewa taurari ne sababi, to wannan shirka ce karama; domin cewa shi ya danganta ni'imar Allah zuwa waninSa, domin cewa Shi – tsarki ya tabbatar maSa – bai sanya taurari sababi ba.

**----------------------------------------------**

**TAMABAYA TA 70: Menene dalili akan haramcin neman shayar da ruwa da masaukan taurari?**

**AMSA TA 70:** Dalili shine fadin Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: *"Allah – Madaukakin sarki – Ya ce: Wanda ya ce: Anyi mana ruwa da falalar Allah da rahamarSa; to wannan mai imani da Nine kuma mai kafircewa taurari, amma wanda ya ce: Anyi mana ruwa da masaukin tauraro kaza da kaza, to wannan ya kafirce Mini kuma yayi imani da taurari".* Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 71: Menen hukuncin gina masallatai akan kaburbura?**

**AMSA TA 71:** Haramun ne, kuma shi tsani ne na shirka, Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: *"Allah Ya tsinewa yahudawa da nasara, sun riki kaburburan Annabawansu masallatai"* Bukhari ne ya ruwaitoshi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 72: Menene tabarruki?**

**AMSA TA 72:** Tabarruki: Shine neman albarka, albarka itace samun alheri da dawwamarsa.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 73: Menene rabe-raben tabarruki?**

**AMSA TA 73:** 1- Tabarrukin da aka shara'anta: Shine wanda ya halatta, shine wanda dalilai daga al-Kur'ani da sunna suka shiryar akansa.

2- Tabarrukin da aka hana: Shine wanda aka haramta.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 74: Menene nau'ikan tabarrukin da aka shara'anta?**

**AMSA TA 74:** Tabarrukin da aka shara'anta nau'i biyu ne:

1- Tabarruki da abubuwa na madda wadanda ake gani; kamar tabarruki da ruwan zamzam.
2- Tabarruki da ayyuka na gari; Kamar sallah da addu'a da sadaka.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 75: Menene nau'ikan tabarrukin da aka hana?**

**AMSA TA 75:** Tabarrukin da aka hana nau'i biyu ne:

1- Wanda shari'a tayi hani daga gare shi; kamar hani daga tabarruki da gumaka da mutum-mutumi.
2- Wanda ya kasance daga sabubban na dimuwa wadanda basu da wata hakika; kamar tabarruki da zatin salihai, ko tufafinsu ko yawunsu, ko bishiyoyi ko duwatsu.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 76: Menene rabe-raben tawassuli a cikin addu'a?**

**AMSA TA 76:** Tawassuli a cikin addu'a ya rabu gida biyu:

1- Tawassulin da aka shara'anta: Shine tawassulin da dalilai na shari'a suka shiryar akansa.
2- Tawassulin da aka hana: Shine tawassulin da dalilai na shari'a basu shiryar a kansa ba, ko sukayi hani daga gare shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 77: Menene nau'ikan tawassulin da aka shara'anta a cikin addu'a?**

**AMSA TA 77:** Tawassulin da aka shara'anta a cikin addu'a nau'i uku ne:

1- Tawassuli da sunayen Allah da siffofinSa; kamar ka ce: Ya Rahmanu Kayi mini rahama.
2- Tawassuli da aiki na gari; kamar fadin Allah – Madaukakin sarki -: ***{Ya Ubanginmu lallai cewa mu munyi imani Ka gafarta mana zunubanmu ka karemu da azabar wuta}*** [Aal-Imran: 16].
3- Tawassuli da neman addu'a daga mutum na gari rayayye wanda yake a halarce, kamar yanda Ukasha – Allah Ya yarda da shi – ya aikata lokacin da ya nemi Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – yayi masa addu'a ya zama daga mutum dubu saba'in wadanda zasu shiga aljanna ba tare da hisabi ba, sai Ukasha dan Mihsan ya ce: Ya Manzon Allah, ka roka min Allah Ya sanyani daga cikinsu, sai Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: *"Kai kana daga cikinsu"* An hadu akansa.

--------------------------------------------

**TAMABAYA TA 78: Menene nau'ikan tawassulin da aka hana a cikin addu'a?**

**AMSA TA 78:** 1- Tawassulu na shirka: Shine tawassulin da shirka da Allah ta shiga cikinsa; kamar neman agaji da salihai da rokonsu koma bayan Allah; kamar fadinsu: Madadi ya Manzon Allah, ko madadi ya Jilani.

2-Tawassuli na bidi'a: Shine tawassuli ta hanyar da dalilai na shari'a basuyi nuni akansu ba; domin cewa tawassuli ibada ne, dan haka wani

abu a cikinta baya halatta sai da dalili na shari'a, daga cikin tawassuli na bidi'a: Tawassuli da zatikan salihai ko alfarmarsu.

----------------------------------------------

**TAMABAYA TA 79: Mecece ceton da zata kasance a ranar lahira?**

**AMSA TA 79:** Shine tsani a wurin Allah da jawo anfani ga wani, ko tunkude cuta daga wani.

----------------------------------------------

**TAMABAYA TA 80: Shin ana neman ceto daga matattu?**

**AMSA TA 80:** Ba'a neman ceto daga matattu; domin cewa ceto mallakin Allah ne Shi kadai, Madaukakin sarki Ya ce: ***{Ka ce ceto gaba dayansa na Allah ne}*** [al-Zumar: 44].

----------------------------------------------

**TAMABAYA TA 81: Menene sharuddan ceto?**

**AMSA TA 81:** Sharuddan ceto biyu ne:

Na farko: Allah Yayi izini ga mai yin ceto yayi ceto, Madaukakin sarki Ya ce: ***{Waye wanda zaiyi ceto a wurinSa sai da izininSa}*** [al-Bakara: 255].

Na biyu: Yardar Allah ga wanda za'a ceta; Madaukakin sarki Ya ce: ***{Kuma baza suyi cetoba sai ga wanda Ya yarda}*** [al-Anbiya: 28].

----------------------------------------------

**TAMABAYA TA 82: Gawa ceto yake kasancewa?**

**AMSA TA 82:** Yana kasancewa ne ga ma'abota Tauhidi, dalili shine fadin Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: *"Mafi azirtar mutane da cetona ranar al-Kiyama wanda ya ce: Babu abin*

*bautawa da gaskiya sai Allah, yana mai tsarkakewa daga zuciyarsa.* Bukhari ne ya ruwaito shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 83: Menene hukuncin wanda ya yiwa Allah – Madaukakin sarki - izgili ko littafinSa ko AddininSa ko ManzonSa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -?**

**AMSA TA 83:** Wanda yayi izgili da wani abu daga hakan; to hukuncinsa cewa shi kafiri ne; Allah – Madaukakin sarki – Ya ce: {Ka ce shin kun kasance kuna izgili ne da Allah da manzonSa* Kada ku kawo wani uzuri hakika kun kafirta bayan imaninku} [al-Taubah: 65,66].

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 84: Menene ma'anar walicci da barranta?**

**AMSA TA 84:** Walicci: Shine soyayya da taimako ga Allah da ManzonSa – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – da kuma musulmai.

Dalili shine fadinSa – Madaukakin sarki -: ***{Kadai masoyinku shine Allah da ManzonSa da wadanda sukayi imani wadanda suke tsaida sallah suke bada zakka alhali su suna masu ruku'u* Wanda ya jibinci Allah da manzonSa da wadanda sukayi imani tolallai rundunar Allah sune masu rinjaye}*** [al-Ma'idah: 55, 56].

Barranta kuma: Shine kin kafirci da kafirai da gaba da su. Dalili shine fadinSa – Madaukakin sarki -: {Hakika abin koyi kyakkyawa ya tabbata gareku game da (Annabi) Ibrahim da wadanda ke tare da shi yayin da suka cewa mutanensu lallai mu mun barranta da ku da abinda kuke bautawa koma bayan Allah mun kafirce muku kuma gaba da kiyayya

sun bayyana tsakaninmu da ku har abada har sai kunyi imani da Allah Shi kadai} [al-Mumtahanah: 4].

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 85: Menene hukuncin taya kafirai murna a idukansu misali idin kirsimeti?**

**AMSA TA 85:** Babban malami Ibu Usaimain – Allah Yayi masa rahama – Ya ce: [Taya kafirai murna a idin Kirsimeti] ko waninsa daga idukan Addini, haramun ne da haduwar malamai, kamar yanda Ibnul Kayyim – Allah Yayi masa rahama - ya cirato a ciukin littafinsa: "Hukunce-hukunce kafiran amana". Fatawowin Ibnu Usaimin (3/44).

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 86: Kayi ta'arifin bidi'a.**

**AMSA TA 86:** Itace yiwa Allah bauta da abinda Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ko sahabbansa ba'akansa suke ba.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 87: Menene hukuncin bidi'a a cikin Addini?**

**AMSA TA 87:** Haramun ce, kuma ita tana daga mafi tsananin sabo.

Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: *"Lallai mafi alherin zance littafin Allah, kuma mafi alherin shiriya shiriyar Annabi Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, mafi sharrin al'amura abubuwan da aka farar, dukkan bidi'a bata ce,"* Muslim ne ya ruwaito shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 88: Shin a Musulunci akwai wata bidi'a kyakkyawa?**

**AMSA TA 88:** Babu wata bidi'a kyakkyawa a cikin Musulunci.

Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: *"Dukkan bidi'a bata ce".* Muslim ne ya ruwaito shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 89: Mecece matsaya daga 'yan bidi'a?**

**AMSA TA 89:** Wajibi shine kiyayar 'yan bidi'a, da gargadarwa daga garesu, da barin zama da su, da duba littattafansu, Ibnu Abbas – Allah Ya yarda da shi – ya ce: (Kada ku zauna da ma'abota son rai, domin zama da su mai jawo cuta a zukata ne). al-Inaba (2/438).

Imama al-Bagawi – Allah Yayi masa rahama – ya ce: (Hakika sahabbai da tabi'ai da masu biye musu da malaman sunnoni sun shude suna masu haduwa akan wannan, masu haduwa akan gaba da 'yan bidi'a da kuma kaurace musu). Sharhus Sunnah (1/127).

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 90: Menene hukuncin barin sallah?**

**AMSA TA 90:** Barin sallah kafirci ne; saboda hadisin Jabir – Allah Ya yarda da shi – ya ce: Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: "Tsakanin mutum da tsakanin shirka da kafirci barin sallah" Muslim ne ya fitar da shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 91: Menene hukuncin kafirta musulmai ba tare da wani hakki ba?**

**AMSA TA 91:** Haramun ne, kuma shi yana daga mafi tsananin zunubai, Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: “Duk mutumin da yacewa dan uwansa: Ya kai kafiri; to hakika dayansu ya koma da ita idan ya kasance kamar yanda yace (to) inba haka bafa zata dawo kansa ne”, Bukhari da Muslim ne suka ruwaoto shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 92: Menene wajibin musulmi a bangaren sahabban Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -?**

**AMSA TA 92:** Wajibi shine sonsu, da kudirce cewa sune mafifitan mutane bayan Annabawa da manzanni – tsira da amincin Allah su tabbata agare su -, da kame harshe daga zance a sha’aninsu sai dai da ambato mai kyau, zagin daya daga sahabbai yana haramta, Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - y ace: “Kada ku zagi sahabbai na, na rantse da wanda raina yake a hannunSa, da ace dayanku zai ciyar da zinari kwatankwacin dutsen Uhudu; bazai kai mudun dayansu ko rabinsa ba”, Bukhari ne ya ruwaito shi.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 93: Menene dalili akan falalar sahabbai – Allah Ya yarda da su -?**

**AMSA TA 93:** Dalili shine fadinSa – Madaukakin sarki -: {Kuma masu tserewa na farko daga Muhajirun da Ansar da wadanda suka biyosu da kyautatawa Allah Ya yarda da su suma sun yarda da Shi, kuma Ya tanadar musu da aljannatai koramu suna gudana a karkashinsu suna

masu dawwama a cikinsu har abada, wancananka shine rabo mai girma} [al-Taubah: 100].

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 94: Waye mafificin sahabbai?**

**AMSA TA 94:** Mafificin sahabbai halifofi hudu, sune: Abubakar al-Siddik, sannan Umar dan Kaddab, sannan Usman dan Affan, sannan Aliyu dan Abu Dalib, sannan ragowar mutane goma wadanda akayi musu bushara da aljanna – Allah Ya yarda da su -.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 95: Me ake nufi da majibnta al'amura/**

**AMSA TA 95:** Sune shugabannin musulmai.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 96: Menene wajibin musulmai bangaren majibinta al'amunsu?**

**AMSA TA 96:** Ji da biyayya inba a sabon Allah bane, da yi musu nasiha, da yi musu addu'a, da barin suka a cikinsu akan munbarai da majalisai, soboda abinda hakan yake haifarwa na fitintinu.

---------------------------------------------

**TAMABAYA TA 97: Menene dalili akan haka?**

**AMSA TA 97:** FadinSa – Madaukakin sarki -: {Yaku wadanda sukayi imani kubi Allah kubi Manzo da majibinta al'amura daga gareku} [al-Nisai: 59]. Da fadin Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -: "Addini nasiha ne. Muka ce: Ga wa ya Manzon Allah? Ya ce: Ga Allah da littafinSa da ManzonSa da shgabannin musulmai da su gaba daya". Muslim ne ya ruwaito shi.

-------------------------------------------

**TAMABAYA TA 98: Yaya nasiha ga shugabannin musulmai zata kasance?**

**AMSA TA 98:** Zata kasance ne a boye, Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – ya ce: "Wanda yake so yayiwa shugaba nasiha to kada ya bayyanar da ita a bayyane, sai dai yayi riko da hannunsa sai ya kebanceta da shi, idan ya karba daga gare shi to hakan, inba haka bafa to ya kasance ya sauke abinda ke kansa". Ahmad ne ya ruwaito shi da waninsa, Albani ya ingantashi da Ibnu Baz – Allah Yayi musu rahama -.

-------------------------------------------

**TAMABAYA TA 99: Menene wajibin musulami a lokacin faruwar fitintinu? Tare da dalili?**

**AMSA TA 99:** Wajibi shine nisantar fitintinu, da lazimtar jama'ar musulmai da jagoransu, da tambayar ma'abota ilimi matabbata a cikin sani.

Dalili fadinSa – Madaukkain sarki -: {Idan wani al'amari yazo musu daga aminci ko tsoro sai su yada shi, da ace sun maida shi zuwa ga Manzo da kuma ma'abota al'amura daga cikinsu da wadanda sukeyin bincikensa daga cikisu zasu sanshi, da badan falalar Allah da rahamarSa gareku ba da kunbi Shaidan sai dai 'yan kadan} [al-Nisai'i: 83].

-------------------------------------------

**TAMABAYA TA 100: Su waye Ahlus Sunnah Wal Jama'a?**

**AMSA TA 100:** Sune masu riko da sunnar Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi – da sahabbansa, da wanda ya bisu ya shiga hanyarsu a cikin kudiri da fada da kuma aikatawa.

Allah yayi dadin tsira yayi aminci ga Annabinmu Muhammad, da alayensa da shabbansa baki daya.

---------------------------------------------

**TUSHE**

**MAFI MUHIMMANCIN TUSHE:**

1- Al-Inabah al-Kubra. Na Ibnu Baddah al-Akbari.
2- Al-Sunnah. Na Imam al-Bagawi.
3- Al-Akidatul Dahawiyya. Na Imam al-Dahawi.
4- Al-Akidatul Wasidiyya. Na Imam Ibnu Taimiyya.
5- Zadul Ma'ad. Na Imam Ibnul Kayyim.
6- Kitabul Tauhid. Na Muhammad Ibnu AbdulWahhab.
7- Al-Usulul salala Wal Kawa'idl Arba'i. na Imam Muhammad Ibnu Abdlwahhab.
8- Majmu'u Fatawa Ibnu Baz. Abdulaziz Ibnu Abdullahi Ibnu Baz.
9- Al-Kaulul Mufid. Muhammad Ibnu Saleh al-Usaimin.
10- Nubzah Fil-Akidatul Islamiyya. Muhammad Ibnu Saleh Ibnu Usaimin.
11- I'anatul Mustafid. Saleh Ibnu Fauzan al-Fauzan.
12- Al-Mulakkhas Fi Sharhit Tauhid. Saleh Ibnu Fauzan al-Fauzan.
13- Al-Mashru'u Wal Mamnu'u Minal Tawassul. Abdussalam al-Barjas.
14- Hukukun Nabiyyi – Sallallahu Alaihi Wasallam – Ala Ummatihi. Sa'id Ibnu Aliyu ibnu Wahb al-Kahdani.

## ABUBUWAN DA LITTAFIN YA KUNSA

Gabatarwar fadilatus Sheikh Saleh Ibnu Fauzan al-Fauzan…………….4

Gabatarwar mawallafi……………………………………………..…….5

***Tambaya ta 1:*** Me yasa muke karanata Tauhidi?………………………6

***Tambaya ta 2:*** Daga ina zamu dauki Akidarmu?…………..…………..6

***Tambaya ta 3:*** Menene Tushe uku wadanda saninsu yake wajaba akan mutum, kuma wadanda za'ayi tambaya game da su a cikin kabari?........6

***Tambaya ta 4:*** Waye Ubangijinka?……………..………………………6

***Tambaya ta 5:*** Da me kasan Ubangijinka?.............................................7

***Tambaya ta 6:*** Ina Allah Yake?..............................................................7

***Tambaya ta 7:*** Menene dalili daga al-Kur'ani akan cewa Allah – tsarki ya tabbatar maSa – Yana sama kuma Shi yana kan al-Arshi?.................7

***Tambaya ta 8:*** Menene ma'anar (Ya daidaita)?......................................7

***Tambaya ta 9:*** Saboda me Allah Ya halicci aljani da mutum?................8

***Tambaya ta 10:*** Menene dalili daga al-Kur'ani akan cewa Allah Ya halicci aljani da mutum dan bautarSa?…………..…………………….8

***Tambaya ta 11:*** Menene ma'anar (Su bauta miNi)?................................8

***Tambaya ta 12:*** Mecece ibada?...........................................................8

***Tambaya ta 13:*** Menene ma'anar shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah?……………………………………………………….8

***Tambaya ta 14:*** Menene ma'anar shaidawa Annabi Muhammad Manzon Allah ne?…………………..……………………………………….8

***Tambaya ta 15:*** Menene mafi girman abinda Allah – Madaukakin sarki - Yayi umarni da shi?..........................................................................9

***Tambaya ta 16:*** Menene rabe-raben Tauhidi?.........................................9

***Tambaya ta 17:*** Menene ta'arifin Tauhidir Rububiyyah?........................9

***Tambaya ta 18:*** Menene ta'arifn Tauhidi Uluhiyya?...............................9

***Tambaya ta 19:*** Menene ta'arifin Tauhidin sunaye da siffofi?..............10

***Tambaya ta 20:*** Ka ambaci wasu daga nau'ikan ibada………...…..…10

***Tambaya ta 21:*** Menene mafi girman abinda Allah yayi hani daga gareshi?.............................................................................................10

***Tambaya ta 22:*** Menene nau'ikan shirka?............................................10

***Tambaya ta 23:*** Yaushe ne shirka farko ta afku a cikin mutane?..........11

***Tambaya ta 24:*** Menene sababin afkuwar shirka a cikin mutanen Annabi Nuhu – amnci ya tabbata agare shi -?......................................11

***Tambaya ta 25:*** Menene ma'anar wuce gona da ir a sha'anin salihai?..11

***Tambaya ta 26:*** Menene hukuncin kiran matattu?................................12

***Tambaya ta 27:*** Shin rokon Allah yana bukatar tsanin wani?................12

***Tambaya ta 28:*** Shin matattu suna amsa kira?......................................12

***Tambaya ta 29:*** Dan wa zamuyi yanka kuma muyi sallah?...................12

***Tambaya ta 30:*** Menene hukuncin yanka da sujjada ga wanin Allah?..13

***Tambaya ta 31:*** Menene hukuncin rantsuwa da wanin Allah,?.............13

***Tambaya ta 32:*** Menene wajibi akan Musulmi a bangaren sunayen Allah?..............................................................................................13

***Tambaya ta 33:*** Meye dalili daga al-Kur'ani akan cewa siffofin Allah basa kama da siffofinmu?....................................................................14

***Tambaya ta 34:*** Menene Addininka?..................................................14

***Tambaya ta 35:*** Shin Allah Yana karbar wanin Addinin da ba Musulunci ba?..........................................................................14

***Tambaya ta 36:*** Menene ta'arifin Musulunci?.....................................14

***Tambaya ta 37:*** Menene rukunan muslunci?.......................................15

***Tambaya ta 38:*** Menene ta'arifin imani?...........................................15

***Tambaya ta 39:*** Menene rukunan imani?...........................................15

***Tambaya ta 40:*** Su waye mala'iku?....................................................15

***Tambaya ta 41:*** Menene hukuncin imani da mala'iku?.........................16

***Tambaya ta 42:*** Waye mafificin mala'iku?..........................................16

***Tambaya ta 43:*** Wadan nene littattafan sama?.....................................16

***Tambaya ta 44:*** Menene hukuncin imani da littattafai?.........................16

***Tambaya ta 45:*** Wannene mafi girman littattafan sama?.......................16

***Tambaya ta 46:*** Mecece ranar lahira?.................................................17

***Tambaya ta 47:*** Menene hukuncin imani da ranar lahira?.....................17

***Tambaya ta 48:*** Menene ma'anar imani da kaddara?............................17

***Tambaya ta 49:*** Menene hukuncin imani da kaddara?..........................17

***Tambaya ta 50:*** Menene kyautayi?....................................................17

***Tambaya ta 51:*** Menene ta'arifin riya?................................................17

***Tambaya ta 52:*** Menene hukuncin riya?..............................................18

***Tambaya ta 53:*** Waye Annabinka?....................................................18

***Tambaya ta 54:*** Menene mafi girman dalilan Annabcinsa……………18

***Tambaya ta 55:*** Menene mafi girman hakkokin Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -?..................................................19

***Tambaya ta 56:*** Menene tsafi?..........................................................19

***Tambaya ta 57:*** Menene bokanci?......................................................19

***Tambaya ta 58:*** Waye dan duba?........................................................19

***Tambaya ta 59:*** Menene hukuncin tafiya wajen dan duba?...................20

***Tambaya ta 60:*** Menene hukuncin tsafi da koyansa?............................20

***Tambaya ta 61:*** Menene hukuncin karanta burujan rabo?.....................21

***Tambaya ta 62:*** Menene ta'arifin layu?...............................................21

***Tambaya ta 63:*** Menene hukuncin layu?..............................................21

***Tambaya ta 64:*** Menene tawada ta shari'a, menene hukuncinsu?.........22

***Tambaya ta 65:*** Menene canfi?...........................................................23

***Tambaya ta 66:*** Menene hukuncinsa? Tare da dalili…………………23

***Tambaya ta 67:*** Shin canfi yana faruwa ba tare da tsuntsaye ba?..........23

***Tambaya ta 68:*** Menene ma'anar neman shayarwa da masaukan taurari?..........................................................................................23

***Tambaya ta 69:*** Menene hukuncin neman shayar da ruwa da masaukan taurari?..........................................................................................23

***Tambaya ta 70:*** Menene dalili akan haramcin neman shayarwa da taurari?.........................................................................................24

***Tambaya ta 71:*** Menene hukuncin gina masallatai akan Kaburbura?...24

***Tambaya ta 72:*** Menene ma'anar tabarruki?........................................24

***Tambaya ta 73:*** Menene rabe-raben tabarruki?....................................24

***Tambaya ta 74:*** Menene nau'ikan tabarrukin da aka shara'anta?..........25

***Tambaya ta 75:*** Menene nau'ikan tabarrukin da aka hana?...................25

***Tambaya ta 76:*** Menene rabe-raben tawassuli a cikin addu'a?............25

***Tambaya ta 77:*** Menene nau'ikan tawassulin da aka shara'anta a cikin addu'a?.........................................................................................26

***Tambaya ta 78:*** Menene nau'ikan tawassuli da aka hana a cikin addu'a?.........................................................................................26

***Tambaya ta 79:*** Menene ceton da zai kasance ranar alkiyama?............27

***Tambaya ta 80:*** Shin ana iya nemna ceto daga matattu?.......................27

***Tambaya ta 81:*** Menene sharuddan ceto?...........................................27

***Tambaya ta 82:*** Gawa ceto zai kasance?.............................................27

***Tambaya ta 83:*** Menene hukuncin wanda yayiwa (S.W.T) izgili?........28

***Tambaya ta 84:*** Menene ma'anar walicci da barranta?..........................28

***Tambaya ta 85:*** Menene hukuncin taya kafirai murna a idukansu?.......29

***Tambaya ta 86:*** Kayi ta'arifin bidi'a…………………………………….29

***Tambaya ta 87:*** Menene hukuncin bidi'a a cikin Addini?.....................29

***Tambaya ta 88:*** Shin a Musulunci akwai wata bidi'a kyakkyawa?.......30

***Tambaya ta 89:*** Menenene matsaya daga ‘yan bidi’a?…………………30

***Tambaya ta 90:*** Menene hukuncin barin sallah?....................................30

***Tambaya ta 91*** Menene hukuncin kafirta musulmai ba tare da wani hakki ba?..........................................................................................31

***Tambaya ta 92:*** Menene wajibin musulmi a bangaren sahabbai?..........31

***Tambaya ta 93:*** Menene dalili akan falalar sahabbai (R.A)?.................31

***Tambaya ta 94:*** Waye mafificin sahabbai?..........................................32

***Tambaya ta 95:*** Me ake nufi da Majibninta al’amura?..........................32

***Tambaya ta 96:*** Menene wajibin musulmai bangaren majibinta ala’amuransu?...................................................................................32

***Tambaya ta 97:*** Meye dalili akan haka?...............................................32

***Tambaya ta 98:*** Yaya nasiha ga shugabannin musulmai zata kasance?...........................................................................................33

***Tambaya ta 99:*** Menene wajibin musulmi a lokacin faruwar fitintinu? Tare da dalili?...................................................................................33

***Tambaya ta 100:*** Su waye Ahlus Sunnah Wal Jama’a?.........................34

**Tushe**……………………..…………………………………………35